# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Ishaya ya Hangi Nesa



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Jonathan Hay**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Mary-Anne S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

Ishaya annabi ne. Aikinsa shi ne ya gaya wa mutane abin da Allah ya ce. Mutane ba sa so su ji Kalmar Allah, amma Ishaya bai ba wa Allah kunya ba.



**Ishaya ya yi wa’azi a lokacin da sarakuna hudu sun yi mulki a lokatai dabam-dabam.**



Sarki Uzziya ya yi mulki a kan Yahuda daga birnin Urushalima. Da farko, Allah ya albarkace Uzziya saboda ya yi abin da yake daidai a gaban UBANGIJI. Amma can an jima Uzziya ya kasance da dagan kai sai ya bar yin wa Allah biyayya. Ya zama kuturu sai da ya kasance shi kadai har mutuwarsa.



Sarki Uzziya ya yi mulki fiye da shekaru 60. Bayan da ya mutu, dansa Yotam ya dauki matsayinsa ya yi mulki na shekaru goma sha bakwai.  Allah ya albarkace Yotam saboda ya saurare duk abin da Allah yake so ya fada ta wurin annabi Ishaya da sauran annabawan.



**Yaron Sarki Yotam shi ne Ahaz. Ahaz yana da shekaru ashirin sa'ad da ya fara mulki, kuma ya yi mulki shekaru goma sha shida a Urushalima. Ahaz bai damu da Allah ba. Ya yi sujada ga gumaka da allolin karya, ya kuma sa mutanen Allah masu yawa su yi haka. KO da yake Ishaya ya ja masa kunne, Ahaz bai saurare gargadin Allah ba. Ya mutu yana da shekaru talatin da biyar (35) ne kawai.**





**Allah ya albarkace sarki na biye, Hezekiya, saboda ya kawar da gumaka da allolin karya, ya yi addu'a ga Allah na gaske. Sa'ad da sojojin abokan gaba suka kai wa Yahuda hari, Hezkiya ya sani sojojinsa ba su da karfin cin nasara. Sai ya tambaye Ishaya ya yi wa Allah addu'ar neman taimako.**

Ishaya ya aika da wannan sako zuwa ga Sarki. “Ga abin da UBANGIJI yake cewa: Kada ka ji tsoron abokin gaba nan… Zan sa ya fadi…” Bayan haka, sai Allah ya sa sojojin abokin gaba suka koma ba tare da sun yi fada da Hezekiya ba.



Ko da yake mutane da yawa kewaye da shi ba sa tunani game da Allah sosai,



Ishaya ya yi tunanin game da shi sosai. Wata rana, ya ga wahayi wanda kamar mafarki ne kuma ba wai kana barci ne ba. A cikin wahayin, Ishaya ya ga yadda daukaka da tsarkin UBANGIJI yake.

“Wane ne zan aika?” Allah ya tambaya a wahayin. “Ga Ni nan. Ka aike ni,” Ishaya ya amsa. Yana a shirye ya yi duk abin Allah ya ce ya yi, ya kuma tafi duk inda Allah ya aike shi.





Watakila Ishaya yana zato Allah zai aike shi zuwa wani wuri mai nesa ga wadansu mutanen da ba su taba ji game da Allah ba. Amma babu, Allah bai yi haka ba. Allah ya gaya wa Ishaya ya yi magana ga mutanensa a kasarsa. Dole ya gaya musu cewa Allah yana bakin ciki saboda zunubansu.



Akwai wadansu abubuwa kuma wadanda Ishaya zai gaya wa mutanensa – abubuwa masu ban mamaki game da Wani wanda zai zama mai kubutarwa mai karfi wanda zai zo domin ya cece mutane daga zunubansu da kuma abokan gabansu.



**Yahudawa suna kira wannan Wani “Meshiya”. Ko da yake suna sa rai Allah zai aiko da Mai ceto, yawanci sun yi rayuwa kamar ba zai zo ba.**



Duka abubuwan da Ishaya ya fada game da Mai Ceton suna nan a cikin littafinsa.  Ko da yake ya rubuta wadannan abubuwa shekaru dari bisa darin da suka wuce kafin suka faru, duka abubuwan da Ishaya ya fada game da Mai Ceton za su zama gaskiya.



Ishaya ya ce Allah da kansa
zai ba da alama.  Ya ce,
“Gashi budurwa za
ta haifi da



sai a kira sunansa Immanuwel.”
Mutane sun sani Ishaya yana
magana game da Mai Ceto na
Allah saboda babu yadda
mace za ta kasance
budurwa har kuma
ta haifi yaro.



Kuma, ma’anar sunan
Immanuwel shi ne
Allah tare da mu!



**“A gare mu an haifi Jariri, a garemu an ba da Da; duka gwamnati za ta kasance a kafadarsa. Sunansa zai zama, Abin mamaki, Mashawarci, Allah Mai Iko, Uba Madawwami, Sarkin Salama.” Ishaya yana da tabbaci cewa Alkawaran Allah za su kasance da gaske, ya yi magana kamar abin ya riga ya faru. Wannan shi ne ake ce da shi annabci.**

Ishaya ya ce Mai Ceton zai zamam mai girma kuma zai aikata ayyuka masu girma. Allah ya kuma gaya wa Ishaya ya gaya wa mutanen cewa Mai Ceton zai sha wahala har a kashe shi. Watakila Ishaya ya yi tunani cewa, yaya za a ce Mai Ceto zai kasance da girma da iko amma zai kasance mai mara karfi da rauni. Amma Ishaya bai yi makagara da Allah – shi dai ya nanata abin da Allah ya aike shi ya fada. Allah zai tabbata annabcinsa ya cika.



**Mai Ceto yana zuwa – ba wai wa Yahudawa kadai ba. Allah ya gaya wa Ishaya cewa Mai Ceton zai zama “haske ga al’ummai”. Al’ummai su ne wadanda ba Yahudawa ba. Allah yana son kowa dakowa kuma Mai Cetonsa zai zo don ya albarkace kowa da kowa ya kuma kawo ceto zuwa ga kowane bangaren duniya.**



# Ishaya ya Hangi Nesa

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Ishaya 1, 6, 7, 9, 53**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

27

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**